


Dila da Kura

Littafin karatu a sauƙaƙe - Mataki na 3

Hausa

Zuwa ga malamai da iyaye:

Kafin a fara amfani da wannan tsarin  koyon karatu, dole sai ɗalibi ya: •    San amon sautukan haruffan Hausa; •    Iya gane kalmomin da aka saba da su.

Dila da Kura


Hausa Nigeria

Copyright © 2017, Enabling Writers Project -American University of Nigeria

http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/
http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye haƙƙin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su. ISBN

Grace Malgwi Writing Trainer/Collection Editor
Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa Hausa Language Consultants
Nas Yakubu Bloom Trainer
Story Writers Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi
Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0 Copyright: SIL International 2009







Gata nan gata nan ku.
A fadar zaki akwai dabbobi da dama.
Akwai kura da dila.
Akwai zomo da biri.

Akwai dabbobin daban-daban a fadar zaki.
In an tashi fada akan yi addu'a.











Addu'ar Dila kullum daban ce.
Addu'ar kariya daga sharri Dila ke yi.
Ashe hakan na ba wa Kura haushi.

Wata rana dila ya yi
wa kura makirci.
Dila ya kawo wa zaki nakiya.



Sarki zaki ya ji daɗin nakiya.
Ya tambaya a ina Dila ya samo.









Dila ya ce kashin kura ne.


Zaki ya sa a nemo kura.
Don ta masa kashin mai daɗi.
Kura ta ce kashinta ba daɗi.
Zaki ya ce ƙarya kura take yi.




Zaki ya sa kura ta yi kashi.
Kura ta yi kashi mai warin gaske.
Zaki ya fusata matuka
Zaki ya yi wa kura duka.
Kura ta suma.



Kura ta farfaɗo.
Kura ta nemi gidan Dila.
Ta ce Dila ya yi mata addu'a.
Kura ta nemi addu'ar kariya daga sharri.





ALL CHILDREN READING: A GRAND CHALLENGE FOR DEVELOPMENT

USAID FROM THE AMERICAN PEOPLE

World Vision

Australian Aid

GLOBAL READING NETWORK